**Wasu matasa mata 14 a garin Girei da ke kusa da Yola a Jihar Adamawan Najeriya sun taka rawar gani a wasu tarukan bita da suka mayar da hankali kan abin da ayyukan mata matasa ya ƙunsa da kalubalen da suke fuskanta idan suka hada aiki da neman ilimi.**

**Daga:**

**Amara Gambo, Maryam One,**

**Aisha One, Amina Mohammed ,**

**Habiba Hassan, Hassana HammaAdama, Maryam Two, Ramatu Bello, Zainab Mohammed,**

**Zaituna Ibrahim, Aisha Musa,**

**Amina Mohammed A, Rabi Musa,**

**Madina Adamu**

**Youth, Gender and Education: Changing Landscapes of Work in Rural Sub-Saharan Africa (WE-SAY) Project:** *Modibbo Adama Univesity, Yola, Nigeria. www.mau.edu.ng*





# Muna da ta Cewa



Mu mata matasa muna da ta cewa, kada ku danne muryarmu; muna da 'yancin a saurare mu da kuma 'yancin samun dama kamar na maza

**Muna Da ta Cewa**

**Halin da ake ciki**

A al'ummar Girei, mata matasa suna gudanar da sana'o'i daban-daban, kamar talla, jaura, koyarwa da dai sauransu, matasan matan suna hada neman kudi da karatu saboda rashin ƙarfin tattalin arzikin, al'adu da ƙai'dojin zamantakewa, rashin son yin aiki daga ɓangaren maza, yawan ayyukan gida, da yawan nauye-nauyen iyali, rikicin cikin gida, cin zarafi daga malamansu a makarantu da kuma a wurin aiki. Hakan kuma ya zame musu wata damuwa tare da iyakance burinsu na aiki da neman ilimi.

**Matsaloli**

A cikin al'ummarmu mata ba su da wata damar faɗa aji ko bayyana ra'ayi kan batutuwan da suka shafi aiki, neman ilimi da kuma al'amarin iyali, ana ganin mata a matsayin ƙasƙantattu saboda al'adun gargajiya, wani lokacin kuma, ana yiwa matan su yi aure tun suna kanana kana hakan na tauye musu damar zuwa makaranta da yin aiki. Bugu da ƙari kuma, ƙarin mata matasa suna fuskantar nau'o'in ƙalubale kamar fyade, tashin hankali a gida, (yunƙurin yin lalata, yin garkuwa da su, wariyar jinsi da rashin tallafi/taimako daga dangi da iyali. An yi amannar cewa matasan mata ba su da murya ko da a game da ilimin, aiki da kuma batun aurensu wanda hakan ya yi matukar tasiri a zamantakewar mu a matsayinmu na matasan mata, kuma al'umma ba ta damu da kulawa da hakan ba.

**Mafita**

Ya kamata malaman addini su tunatar da maza game da abin da Musulunci ya koyar da yadda za su tafiyar da rayuwarsu.

Yakamata a hana auren wuri

Yakamata a ɗau matakan hana tallace-tallacen mata da yara kanana akan tituna.

Haka kuma maza su tsaya muƙamin su na uba su ɗauki nauyin karatu da biyan kudin makaranta da sauran buƙatu tare da kuma ciyar da iyali.

Ya kamata maza su fahimci mata dangane da (bukatunsu) a duk lokacin da su (mata) suka gaji

Lallai ne matasa mata su samu goyon baya daga maza, iyaye da kuma al'umma don samun damar yin ilimi mai zurfi.

Ya kamata a matsayin mu na matasan mata mu dage wajen ci gaba da gudanar da sana'o'inmu domin duk sanda mutum ya dage wajen ganin abubuwa sun sauya to zai iya sauya su.

Kada a sa mata su yi noma don ciyarwa ko kula da iyali

Iyalai su tuntuɓi masana al'amura da zamantakewar aure lokacin da suka fuskanci matsalolin da ba za su iya warwarewa a gida ba

Yakamata a kai rahoto ga 'yan sanda duk sanda aka samu rikicin cikin gida ko yin garkuwa da wata, sannan a dauki mataki kamar yadda doka ta tanada

Maza su sa hannu wajen kula da yara da kuma gudanar da ayyukan gida

Taro/tattaunawar iyali: yayin tattaunawa a tsakanin dangi ana iya magance rinjayen maza akan mata

Yakamata a gina cibiyoyin koyawa matasan mata dabarun sana'a.

Lallai ne al'umma da gwamnati su magance tsohuwar aƙidar nan ta ɗaukar mata a matsayin ƙasƙantattu.